
# Gurbacewar Amfanin Gona ta Hanyar Guba da Kuma Hanyoyin Kamuwa da su




**Guba tana da nau'ika sanannu guda huda: B1, B2, G1 da G2**

**Menene su?**

Su guba ne na halitta wanda *fufuna* ke haifarwa, ciki har da *A. aflatoxiformans*, *A. Parasiticus.* Sun kasance masu iya jure zafi, marasa wari, marasa launi da kuma marasa ganuwa da ido.

*Gurbatacciyar Gyada*




**Menene tasirinsu?**

Suna iya haifar da kansar hanta, canza tsarin sel na jikin dan adam, nakasa yara tun suna ciki, rage karfin fararen sel masu yaki da kwayoyin cuta a jikin dan adam, da kuma rage girman yara.

*Tsuntsaye (kaji) marasa lafiya*



*Ciwon kansar hanta wanda guba ke haifar wa*



*Hoton: : cornell.edu*

**A ina za'a iya samun su?**

Ana samun su a cikin gurbataccen amfanin gona da ake shukawa a yankuna masu zafi haka zarika wurare masu zafi da damshi na duniya.



*Ana iya samun guba M1 (Aflatoxin M1) Wanda aka samo daga guba B1 (aflatoxin B1) a cikin gurbataccen kayan amfanin gona na kaji da na sarrafa madara.*

**Gurbacewar amfanin gona ta hanyar guba (aflatoxin) na faruwa ne sanadiyar gubar fungai (aflatoxin fungi). Gurbacewar na iya faruwa:**

- **Kafin Girbi:** A lokacin da fungai ke shiga ta gemun masara, tsagewa da ramukan kwari a cikin shukan.
- **Lokacin Girbi:** A lokacin da aka sanya amfanin gona kai tsaye a kasa, ko aka yi sussuka mara kyau, fungai daga kasa ko iska na iya siga cikin hatsin da suka lalace.
- **Bayan Girbi:** A lokacin da aka adana ko ake jigilar hatsin a cikin yanayi na rashin tsafta fungai (fungi) daga kasa ko iska na iya shiga.

## Yanayin dake kara habakar gurbataccen guba.



Kasuwanni marasa tsari, inda ake siyar da kayan abinci da yawa ba tare da fakitin kariya ba.




Jigilar kayayyaki cikin yanayi mai karancin inganci.




Rashin isasshen kulawa don kwari

A lokacin da ayyukan noma, stare stare bayan girbi, adanawar amfanin gona, yanayin jigilar kayan amfanin gona da wurin kasuwanci na amfanin gonar na da karancin infanci, amfanin gonar sau da yawa na cikin hatsarin kamuwa da gubar fungai. Wadannan fungai masu cutarwa ne ke haifar da guba a cikin abinci.



Karancin ingantatcen yanayin ajiya da adanawa.



Rashin kulawa bayan girbi

## Magance Gubar Yana da Mahimmanci!

**Fa'idodin lafiyayun kayayaki da basa dauke da guba :**

- Kara damar samun abinci lafiyayyu.
- Babu wata illa ga lafiyar dan adam da ta dabbobi daga cin lafiyayyun hatsi.
- Kara damar fitarwa kasashen waje saboda ingancin amfanin gonar ya cika ka'idoji.








# Dabarun Magance Guba Kafin Girbi:

**Kauce wa biotic danniya kamar gina jiki da kuma ruwa danniya da:**

- Guji matsaloli kamar rashin sunadari da ruwa ta hanyar dasa ko shuka mafi dacewa ko ingantattun iri.
- Tabbatar da samun sunadari ma shuka ta hanyar cire ciyayi akan lokaci da saka taki.

**Kauce wa biotic danniya daga kwari da kuma pathogens da:**

- Guji matsalar kwari da kwayoyin cuta ta hanyar yin amfani da tsarin shuka amfanin gona daban daban ko wacce kaka don rage A. flavus da sauran fungai masu haifar da guba.
- Yin amfani da dabarun magance kwari masu dacewa.
- Yin amfani da Aflasafe™ don magance gubar fufuna kafin girbi.

# Dabarun Magance Guba a Lokacin Girbi da Bayan Girbi



Tabbatar da an girbe amfanin gona a kan lokaci sannan kuma a tabbatar da amfanin gona na a bushe a lokacin girbi ta hanyar gujewa sake jikewa daga ruwan sama.



Girbe amfanin gona kai tsaye cikin jakunkuna (buhuna) ko ajiyewa a kan shimfida a kasa. A ware wadanda suka lalace don jefarwa.



Yi tsibi na runbuna hatsi da kyau don bada damar gudun ruwa mai kyau, wanda ba ya bari ruwa ya taru kuma ya samar da wuraren habakar gubar.





Bushar a kan wuri da aka rufe da shimfida ko madaukakiyar dandami, ba kai tsaye a kasa ba. A bushar zuwa < 9 % (gyada) da < 13 % (masara) masu damshi. A zabe hatsin da suka lalace, canza launi da wadanda kwari suka lalata.



Ajiye busassun hatsi yadda ya kamata a kyawawan wuraren ajiya, nesa da kwari, tare da iskar da ta dace, akan wurin ajiya, da kuma nesa da bango.






Yi jigilar hatsi a kyakkyawar yanayi na tsafta a cikin manyan motoci a rufe, a kuma daura hatsin kan katako (pallet). A guji huda jakunkuna ko buhuna yayin lodawa da saukewa daga manyar motoci da kuma a lokacin tafiya.

Chibiyar kula da ayyukan noma ta kasa (IITA) tare da hadin gwiwar ma'aikatar noma da raya Karkara ta tarayya tare da tallafi daga hukumar abinci da noma ta majalisar dinkin duniya ne suka shirya wannan rubutatcen bayani, ilimantarwa da sadarwa.